


# Fansa daga La'ana

*An maida Yesu la'ana domin mu shiga cikin albarka*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Bari mu dubi yanayi da kuma iyakar fansarmu ta wurin Kristi. Ayar mu ta yau ita ce Galatiyawa 3:13–14:

> "Kristi ya fanshe mu daga la'anar nan ta Shari'a, da ya zama abin la'ana saboda mu—domin a rubuce yake cewa, 'Duk wanda aka kafa a jikin itace La'ananne ne '— an yi wannan kuwa domin albarkar nan da aka yi wa Ibrahim ta saukar wa al'ummomi ta wurin Kristi Yesu, mu kuma ta hanyar bangaskiya mu sami Ruhun nan da aka yi alkawari."

A nan Bulus yana magana a kan dokar Musa, wadda aka yi cikakken bayanin ta a cikin littafin Kubawar Shari'a, inda Allah ya ce duk wanda aka kashe ta hanyar ratayewa a kan itace la'ananne ne. Kalmar itace kuma tana nufin wani itacen da ake yin giciye da shi. Shaidar cewa irin wannan mutumin na karkashin la'ana shi ne cewa yana rataye a kan itace a bainar jama'a.

Domin a fanshe mu daga la'anar shari'a, Kristi ya zama la'ana a madadin mu. An nuna wannan a fili lokacin da aka rataye shi a kan gicciye. Ya zama dole a gare shi ya zama la'ana domin la'anar Allah na kan dukan zunubi da rashin biyayya ga Allah.

Asirin abin da ya faru a kan gicciye shi ne cewa akwai musayar da Allah ya shirya—wani abu ne da ido na halitta ba zai iya gani ba, amma ana iya fahimtar sa ne kawai ta wajen bayyanawar Allah ta wurin Ruhu Mai Tsarki da kuma Littafi Mai Tsarki. Kristi ya zama la'ana—Ya ɗauki la'anar saboda zunubin mu da kuma rashin biyayya—saboda mu, kuma, ta wurin bangaskiyarmu a gare shi, mu sami damar samun albarkar da ta ke tasa ta wurin biyayyar Sa marar zunubi.

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Ina furta cewa domin a fanshe ni daga la'anar shari'a, Kristi ya zama la'ana a madadi na. An maida Yesu la'ana domin in shiga cikin albarkar. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

**Abincin Yini** ★

Kwafi: WD-B097-121-HAU

Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources

> “Ilimi yana sanya mabuɗin a hannunka, amma bangaskiya ce ke juya mabuɗin a kofar kuma ya buɗe ɗakin taskar wadatar Allah a cikin Almasihu.””
>
> **Derek Prince**

Derekprince.com/ha/resources